جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات

ضيوف الرحمن
hajjumrh.com



ADDU'A DAGA

ALKUR'ANI DA HADISI

Hausa

هوسا

ضيوف الرحمن
hajjumrh.com

شركاء التنفيذ :



دار الإسلام


بيان الإسلام


رواد التراجم


المحتوى الإسلامي

يتاح طباعة هذا الإصدار ونشره بأي وسيلة مع
الالتزام بالإشارة إلى المصدر وعدم التغيير في النص

Tel : +966 50 244 7000
info@islamiccontent.org
Riyadh 13245-2836
www.islamiccontent.org

ADDU'A DAGA AL'KUR'ANI DA HADISI

Godiya ta tabbata ga Allah Shi kadai, tsira da aminci su tabbata ga wanda babu wani Annabi a bayansa.

1 {Da sunan Allah Mai rahama Mai jin kai *
Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai*
Mai yawan rahama Mai yawan jinkai*.
Mamallakin ranar sakamako*.
Kai kadai muke bautawa, kuma gareKa kadai muke neman taimako*.
Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya*.
Hanyar wadanda ka yi ni'ima a garesu, ba wadanda Ka yi fushi a gare su ba, ba kuma batattu ba} Suratul Fatiha, daga ayah ta 1-7



2 {Ya Ubangijiinmu Ka karba mana, Kai mai ji ne kuma masani ne.} Suratul Bakarah, aya ta: 127

3 {Ka karbi tubanmu hakika kai Mai yawan karbar tuba; ne Mai jin kai.} Suratul Bakarah, aya ta: 128

4 {Ya Ubangijinmu Ka bamu kyakkyawa a duniya, kuma Ka bamu kyakkyawa a lahira, Ka kuma kiyayemu azabar wuta.} Suratul Bakara aya ta 201.

5 {Mun ji kuma mun bi, muna neman gafararKa, Ubangijinmu kuma makoma na gareka.} Suratul Bakara, aya ta 285.

6 {Ya Ubangijinmu ! Kada Ka kama mu in muka manta, ko muka yi kuskure, Ya Ubangijin mu ! Kada Ka dora mana nauyi, kamar yadda Ka dora shi akan wadanda suka zo kafin mu, Ya Ubangijinmu ! Kada Ka dora mana abinda ba zamu iya dauka ba, Ka yi mana afuwa, Ka gafarta mana, Ka yi mana rahama, Kai ne Mai jibintar mu, Ka taimake mu akan mutanan da suke kafirai.}

Suratul Bakara, aya ta 286.

7 {Yã Ubangijinmu! Kada Ka karkatar da zukãtanmu bãyan har Kã shiryar da mu, kuma Ka bã mu rahama daga gunKa. Lalle ne, Kai, Kai ne Mai yawan kyauta.} Suratu Ali Imran, aya ta 8.

8 Ya Ubangijinmu ! Lalle ne mu mun yi imani, to Ka gafarta mana zunubammu , Ka tsaremu daga azabar wuta.} Suratu Ali Imaran, aya ta: 16.

9 {Ya Ubangijina Ka yi min baiwa daga gareKa ta zuriya mai albarka, lalle Kai Mai jin Addu'a ne.} Suratu Ali IImran, aya ta: 38.

10 {Yã Ubangijinmu! Mun yi imãni da abin da Ka saukar, kuma mun bi ManzonKa, sai Ka rubũta mu tãre da mãsu shaida.} Suratu Ali Imran, aya ta: 53

11 {Ya Ubangijinmu! Ka gafarta mana zunubammu da barnarmu a lamuran mu, Ka tabbatar da duga-dugammu, Ka taimaka mana akan mutanan da suke kafirai.} Suratu Ali Imran, aya ta: 147.

12 {Ya Ubangijinmu ! Ba Ka halicci wannan (halittar) dan wasa ba, tsarki ya tabbata a gareKa, to Ka tsaremu daga azabar wuta*.

Ya Ubangijinmu lalle kai duk wanda ka shigar wuta lalle Ka kunyatar da shi, azzalumai basu da wasu mataimaka*

Yã Ubangijinmu! Lalle ne mũ mun ji Mai kira yanã kira zuwa ga ĩmãni cẽwa, 'Ku yi ĩmãni da Ubangijinku.' Sai muka yi ĩmãni. Yã Ubangijinmu! Sabõda haka Ka gãfarta mana zunubanmu, kuma Ka kankare miyãgun ayyukanmu daga gare mu. Kuma Ka karɓi rãyukanmu tãre da mutãnen kirki*

Yã Ubangijinmu! Ka bã mu abin da Ka yi mana wa'adi (alkawari) a kan manzanninKa, kuma kada Ka tozarta da mu a Rãnar ¡iyãma. Lalle ne Kai, bã Ka sãɓãwar alkawari.} Suratu Ali Imran, aya ta: 191-194.

13 {Ya Ubangijinmu ! Mun yi imani, to Ka rubuta mu a cikin masu shaidawa.} Suratul Al'ma'idah, aya ta 83.

14 {Ya Ubangijinmu ! Mun zalinci kawunanmu, kuma idan ba Ka gafarta mana ba, ba Ka yi mana rahama ba, tabbas za mu kasance cikin masu asara.} Suratul A'araf, aya ta : 23

15 {Ya Ubangijinmu ! Ka da ka sanya mu tare da azzalumai.}


Suratul A'araf, aya ta: 47.




16 Ya Ubangiji{Kai ne Waliyyinmu, to Ka gafarta mana Ka yi mana rahama, kuma Kai ne fiyayyan masu gafara*.
Ka rubuta mana kyakkyawa a wannan duniyar haka nanma a lahira.} Suratul A'araf, aya ta 155-156.

17 {Allah ya isar mini, babu abin bautawa da cancanta sai shi, a gare shi na dogara, kuma shi ne Ubamgijin Al'Arshi mai girma.} Suratut Taubah, aya ta: 129.

18 {Ya Ubangijinmu ! Ka da ka sanya mu fitina ga mutanan da suke azzalumai *
Kuma ka tserar da mu domin jin kanka daga mutane kafirai.} Suratu Yunus, aya ta: 85-86.





19 {Yã Ubangijina! Lalle ne nĩ, inã nĕman tsari gare Ka da in tambaye Ka abin da bã ni da wani ilmi a kansa. Idan ba Ka gãfarta mini ba, kuma Ka yi mini rahama, zan kasance daga mãsu hasãra.} Suratu Hud, aya ta: 47.

20 {Ya Mahaliccin sammai da kassai, kaine majibinci na a duniya da lahira, Ka karbi raina ina musulmi, kuma ka riskar da ni da managartan bayi.} Surar Yusuf, aya ta: 101 {10}[1]

21 {Ya Ubangijina! Ka sanya wannan gari (Ya zama) amintacce, Ka nisantar da ni da 'ya'yana daga bautar gumaka.}

Suratu Ibrahim, Aya ta: 35.

22 {Yã Ubangijina! Ka sanyã ni mai tsayar da salla. Kuma daga zũriyyata. Yã Ubangijinmu! Kuma Ka karɓi addu'ata.} Suratu Ibrahim, Aya ta: 40.

23 {Yã Ubangijinmu! Ka yi gãfara gare ni, kuma ga mahaifãna, kuma da mũminai, a rãnar da hisãbi yake tsayãwa.} Suratu Ibrahim, Aya ta: 41

24 {Ya Ubangijinmu ! Ka ba mu rahama daga gareka, kuma Ka shirya mana a lamari nan namu abinda yake daidai.}

Suratul Kahf, Aya ta: 10.

25 {Ya Ubangijina ! Ka yalwata min kirjina*
Ka sawwaka min lamari na*.
Ka warware kulli daga harshe na, za su fahimci magana ta.} Suratu Ɗãha, ayoyi na: 25-28.

1-Ka duba don fa'ida: littafin na ibn Kaayyim, shafi na: 436 da 437,

26 {Ya Ubangijina Ka kara min ilimi.} Suratu Taha, Aya: 114.

27 {Babu abin bautawa da gaskiya Sai Kai, tsarki ya tabbata a gareKa, lallai ni na kasance cikin azzalumai.} Suratul Anbiya, aya ta: 87.

28 {Ya Ubangijina kada Ka barni ni kadai, Kai ne kuma fiyayyan masu gajewa.} Suratul Anbiya, aya ta: 89.

29 {Ya Ubangijina ina neman tsarinKa daga zungurin shaidanu *
Kuma inã nẽman tsari da Kai, ya Ubangijĩna! Dõmin kada su halarto ni.} Suratul Mu'uminun, Aya ta: 97-98.

30 {Ya Allah Ubangijinmu ! Mun yi imani, to Ka gafarta mana, Ka ji kanmu, Kai ne fiyayyan masu jin kai.} Suratul Mu'minun, aya ta: 109

31 {Ya Ubangijina Ka gafarta, kuma Ka jikai, Kai ne fiyayyan masu jin kai.} Suratul Muminina, aya ta: 118.





32 **{Ya Ubangijinmu! Ka karkatar da azãbar Jahannama daga gare mu. Lalle ne, azãbarta tã zama tãra))***
Lalle ita (jahannama) ta munana a mazauna da matabbata.}
Suratul Furkan, aya ta: 65-66

33 {**Ya Ubangijinmu !** Ka bamu sanyin idanu daga matanmu da zuriyar mu, kuma Ka sanya mu shugabanni ga masu tsoron Allah.} Suratul Furkan, aya ta: 74.

34 {**Ya Ubangijīna!** Ka ba ni hukunci, kuma Ka riskar da ni ga sãlihai*
Kuma Ka sanya min harshe na gaskiya ga 'yan karshe*
Kuma ka sanya ni daga magadan Aljannar ni'ima.} Suratus Al-Shu'ara, Aya ta: 83-85.

35 {Kuma kada Ka kunyata ni a rãnar da ake tãyar da su *
Ranar da dukiya ba ta amfani haka'ya'ya (su ma ba sa anfani) *
Fãce wanda ya jẽ wa Allah da zũciya mai tsarki.} Suratus Al-Shu'ara, Aya ta: 87-89.

36 {**Ya Ubangijina** Ka kimsa min in godewa ni'imarKa da Ka ni'imtata a gareni, da kuma mahaifana da kuma in yi (aiki) na kwarai da zaKa yarda da shi, kuma Ka sanyani cikin bayinKa na kwarai.} Suratun Namli, Aya ta: 19.

37 {**Ya Ubangijina** lalle ni na zalinci kaina, Ka gafarta mini.}
Suratul Kasas, Aya ta:16.



38 **{Ya Ubangijina Ka tseratar da ni daga mutanan da suke azzalumai.}**
Suratul Kasas, Aya ta : 21.

39 {**Ina fata Allah** Zai shiryar dani hanya madaidaiciya.}
Suratul Kasas, Aya ta: 22.

40 {**Ya Ubangijina** lallai ni mabukacine dangane da abinda Ka saukar zuwa gareni na alheri.} Suratul kasas, aya ta: 24.

41 {**Ya Ubangijina** Ka taimakeni akan mutanan da suke mabarnata.} Suratul Ankabut, Aya ta: 30

42 {**Ya Ubangijīna!** Ka bã ni (abõkin zama) daga sãlihan mutãne.}Suratus Saffat, Aya ta: 100.

43 {**Ya Ubangijina** Ka kimsa min in gode da ni'imarKa wacce Ka ni'imtata ta a gareni da kuma mahaifana da kuma in aikata (aiki) na gari da zaKa yarda da shi, kuma Ka gyara mini a cikin zuriyata, lallai ni na tuba zuwa gareKa kuma lallai ni ina cikin musulmai.} Suratul Ahkaf, Aya ta: 15.

44 {**Yã Ubangijinmu!** Ka yi gãfara a gare mu, kuma ga 'yan'uwanmu, waɗanda da suka riga mu yin ĩmãni, kada Ka sanya wani ƙulli a cikin zukãtanmu ga waɗanda suka yi ĩmãni. Yã Ubangijinmu! Lalle Kai ne Mai tausayi, Mai jin ƙai.}Suratul Hashr, aya ta: 10.

45 {**Ya Ubangijin mu !** GareKa muka dogara, kuma gareKa muka mayar da lamuran mu, kuma makona zuwa gareKa take.} **Suratul Mumtahana, aya ta: 4.**

46 {**Yã Ubangijinmu!** Kada Ka sanya mu fitina ga waɗanda suka kãfirta, kuma Ka yi gãfara gare Mu. Ya Ubangijinmu! Kai ne Mabuwãyi, Mai hikima.} **Suratul Mumtahana, aya ta: 4.**

47 {**Ya Ubangijina** Ka gafarta min da iyayena da kuma wanda ya shiga gidana yana mumini, da muminai (maza) da muminai (mata).} Suratu Nuh, aya ta 28.

48 {**Ya Ubangijin mu !** Ka cika mana hasken mu, Ka gafarta mana, lallai Kai mai iko ne akan komai.} Suratut Tahrim, aya ta: 8.

***



49 “**Ya Allah Ubangiji!** Ka shiryar da ni ga duk abinda suka yi sabani a cikinsa na gaskiya da izininKa, lallai Kai Kana shiryar da wanda Kake so zuwa hanya mikakkiya.”[2]




50 “**Ya Allah** Ka bani hikima, wacce duk wanda aka ba shi ita, to lalle an ba shi alkhairi mai yawa.”.[3]

51 **“Ya Allah** Uabangiji! Ka tabbatar da ni da magana tabbatacciya a rayuwar duniya da lahira.”[4]

2- An dosano daga Suratul Bakara aya ta: 213
3- An ciro daga Suratul Bakara: aya ta: 269.
4- An ciro daga Suratu Ibrahim, aya ta: 27.

52 “Ya Allah Ubangiji ! Ka soyar mana imani, Ka kawata shi a zukatammu, Ka kyamatar mana da kafirci da fasikanci da laifuka, Ka sanya mu cikin masu shiryarwa.”.[5]



5- An ciro daga Suratul Hujurat, aya ta 7

53 **“Ya Ubangiji !** Ka tsare ni yi wa kaina kwauro, Ka sanyani cikin masu rabauta.” [6]

54 **“Ya Allah Ubangiji !** Ka ba mu anan duniya abu mai kyau, a lahira ma abu mai kyau, ka tsaremu azabar wuta.” [7]

55 **“Ya Allah Ubangiji!** ni ina neman tsarinka daga fitinar wuta da azabar wuta, da fitinar kabari, da sharrin fitinar wadata, da sharrin fitinar talauci, Ya Allah ni ina neman tsarinka daga fiitinar Dujal, ya Allah Ubangiji ! Ka wanke zuciyata da ruwan kankara, Ka kuma tsarkake zuciyata daga kurakure, kamar yadda Ka tsarkake farin tufafi daga datti, Ka nisanta tsakanina da tsakanin kurakure na ,kamar yadda Ka nisanta tsakanin gabas da yamma,Ya Allah ni ina neman tsarinka daga lalaci da laifuffuka da bashi.”[8]



6- An ciro daga Suratut Tagabun, aya ta: 16.

7- Bukhari ne ya ruwaito a Hadisi mai lamba 4522, da lamba 6389, da kuma Muslim mai lamba 2690.

8- Bukhari, a lamba 832, da Muslim, mai lamba 589.

56 **“Ya Ubangiji** ni ina neman tsarinka daga gajiyawa, da kasala, da tsoro, da tsufa, da rowa, kuma ina neman tsarinka daga azabar Kabari, kuma ina neman tsarinka daga fitinar rayuwa da ta mutuwa.” [9]

57 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinka daga wahalar bala'i da riskar tsiyata, da mummunan hukunci, da dariyar makiya.”[10]

58 **“(Ya Allah** Ka gyara mini Addinina, wanda shi ne ƙashin bayan al’amarina, kuma Ka gyara mini duniya ta wacce nake rayuwa a cikinta, Ka kuma gyara mini lahira ta wacce a cikinta ne makomata take, ka sanya rayuwa (ta zamo) ƙarin duk wani alheri gareni, kuma Ka sanya mutuwa ta zamo hutu ce a gare ni, daga dukkan wani sharri.”[11]



9-Bukhari, a lamba 2823, da Muslim, mai lamba 2706.

10- Bukhari, a lamba 6347, da Muslm, a lamba 2707, lafazinsa:((Manzan Allah-tsira da amincin allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana neman tsari daga wahalar bala'i da riskar tsiyata, da mummunan hukunci da dariyar makiya)).

11- Muslim ne ya fitar da shi a lamba 2720.

59 **“Ya Allah** ina rokonKa shiriya da tsoron Allah, da kamewa, da wadata.” [12]

60 **“Ya Allah** ina neman tsarinka daga gajiyawa, da kasala, da tsoro da rowa, da tsufa, da azabar kabari, ya Allah Kabawa raina tsoran Allah, Ka tsarkaketa, Kai ne mafificin mai tsarkaketa, Kai ne majibincin lamarinta kuma shugabanta, Ya Allah ina neman tsarinka daga ilimin da bashi da amfani, da zuciyar da bata risina, da ran da baya koshi, da addu'ar da ba'a amsamata.” [13]



12- Muslim ne ya fitar da shi a lamba 2721.

13- Muslim ne ya fitar da shi, a lamba 2722.

61 **“Ya Allah** Ubangiji Ka shiryarda ni Ka kuma datar dani, Ya Allah ni ina rokanka shiriya da dacewa.”[14]

62 “**Ya Allah** ina neman tsarinKa daga gushewar ni'imarKa, da juyawar lafiyarKa, da shammatar azabarKa, da dukkan fushinKa.”[15]

63 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinKa daga sharrin abinda na aikata, da kuma sharrin abinda ban aikatata ba.”[16]

64 **“Ya Allah Ubangiji! Ka yawaita dukiyata, da yayana, Ka yi albarka a gareni cikin abinda Ka bani)), (({kuma Ka tsawaita rayuwata a bisa biyayya gareka, Ka kuma kyautata aikina} Ka gafarta min.”** [17،18]




14- Muslim ne ya fitar da shi a lamba 2725.

15- Muslim ne ya fitar da shi, a lamba 2739.

16- Muslim ne ya fitar da shi, a lamba 2716.

17- Bukhari a cikin Al'adabul al’Mufrad, a lamba ta: 653, kuma Albani ya inganta shi a cikin Silsilatul al'ahadsis Sahiha, a lamba 2241. kuma a cikin Sahihul Al'adabul Mufrad, shafi na 244, fadinsa-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana nuni a gare shi, lokacin da aka tambaye shi: wanene mafificin mutane? sai ya ce:((wanda rayuwarsa ta tsawaita, kuma aikinsa ya kyautata)), Tirmizi, a lamba 2329, haka kuma Ahmad, da lamba 17716, kuma Albani ya ingantashi a cikin Sahihut Tirmizi, 2/271, kuma hakika na tambayi babban malaminmu ibn Baaz -Allah ya yi masa rahama- a bisa yin addu'a da shi, kuma shin hakan sunna ne? sai ya ce: (Eh).

18- Addu'ar annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- da ya yi ga Anas tana nuni a gareta: ((Ya Allah Ka yawaita dukiyarsa, da yayansa, Ka kuma yi albarka a gare shi cikin abinda ka ba shi)). Bukhari, a lamba ta:1982, hakanan Muslim, a lamba 660.



65 “Babu wani abin bautawa da gaskiya sai Allah Mai girma Mai hakuri, babu wani abin bautawa da gaskiya face Allah Ubangijin Al’arshi mai girma, babu wani abin bautawa da gaskiya face Allah Ubangijin sammai kuma Ubangijin kasa kuma Ubangijin Al’arshi mai yawan baiwa.”[19]

66 “Ya Allah rahamarKa nake kauna, kar Ka barni da kaina daidai da kiftawar ido, Ka gyara min al’amura na dukkansu, babu wani abin bautawa da gaskiya sai Kai.”[20]



19- Bukhari, a lamba ta: 6345, da kuma Muslim, a lamba ta: 2730.

20- Abu Dawud, a lamba, 5090, da Ahmad 5/42, kuma albany ya kyautata shi, a cikin Sahih Abi Dawud, 3/250, da Sahihul Al'adabi al’Mufrad, kuma babban malami ibnu Baaz ya kyautata Isnaadinsa, a cikin Tuhfatul al'akhbaar, shafi na: 24.



67 “Babu abin bautawa da gaskiya Sai Kai, tsarki ya tabbata a gareKa, lallai ni na kasance cikin azzalumai.”[21]

68 **“Ya Allah Ubangiji!** ni bawanka ne dan bawanka dan baiwarka, makwarkwadata na hannunka, kaddararka mai zartuwa ce a gareni, hukuncinka adalci ne a gareni, ina rokonka da dukkanin wani suna naka, da Ka ambaci kanKa da shi, ko Ka saukar da shi a cikin littafinka, ko Ka sanar da shi

21-Tirmizi, a lamba ta: 3505, da Hakim, kuma al-zahbi ya inganta shi, 1/505, kuma ALbany ya inganta shi a cikin Sahihut Tirmizi, 3/168, lafazinsa:((Addu'ar zinnun (annabi Yunus) lokacin da ya kira shi, alhali yana cikin kifi: ((cewa babu abin bautawa da gaskiya sai kai, tsarki ya tabbatarmaka, lalle ni na kasance daga cikinazzalumai)). {Al'anbiyaa: 87}, cewa wani mutum musulmi ba zai roki wani abu da ita ba, face sai Allah Ya amsa masa)).

ga wani daga halittarKa ko Ka kadaita da shi a cikin iliminka na gaibu a gurinka, Ka sanya Alkur'ani farin cikin zuciyata, da hasken kirjina, da yayewar bakin cikina, da tafiyar damuwata.” [22]

69

“Ya Allah Ubangiji Mai juya zukata, Ka tabbatar da zukatan mu akan biyayyarka.” [23]

22-Ahmad, 1/391, 452 da Hakim, 1/509, kuma Hafiz ya kyautata shi a cikin Takhrijil, Al’azkaar, kuma Albany ya inganta shi a cikin Takhrijil kalami Dayyib, shafi na 73.
23- Muslim, a lamba ta 2654.

70 “Ya Mai juya zukata, Ka tabbatar da zuciyata akan addininKa.” [24]

71 **“Ya Allah ni ina rokanKa lafiya a duniya da lahira.”** [25]



72 **“Ya Allah** Ka kyautata karshenmu adukkannin al'amura, Ka tserar da mu daga kunyatar duniya da azabar lahira.” [26]

73 **Ya Ubamgiji!** Ka taimakeni, kada ka taimakawa wani a kaina (ka datar dani ambatonka), kada Ka bawa wanda zai hanani biyayyarKa rinjaye a kaina, Ka taimakeni (akan kafirai makiya addininKa), kada Ka dora wani daga halittarka a kaina, Ka riskar da makircinka ga makiyana (Ka azurtani dabarar kubuta daga sharrinsu),

24-Tirmizi, a lamba ta 3522, da Ahmad, 4/182, da Hakim, 1/525, da 528, al-Zahabi kuma ya inganta shi, Albany ma ya inganta shi a Sahihul Al-jami;i, 6/309, kuma Tirmizi ya inganta shi, 3/171. Hakika Ummu Salama-Allah ya yarda da ita ta ce: ((Mafi yawan addu'arsa-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ta kasance)).

25- Tirmizi, a lamba 3514, da Bukhari a cikin Al-adabul Al’mufrad, a lamba 726, lafazinsa a gurin Tirmizi: ((Ku roki Allah lafiya a duniya da lahira)), a wani lafazin kuma: ((Ku roki Allah rangwami da lafiya, hakika ba'a bawa wani (wani abu ba) bayan rai mafi alkhairi fiye da lafiya)), lalle Albany ya inganta shi a cikin Sahihul Ibnu Majah, 3/180, da 3/ 185, da 3 170, kuma yana da SHAWAHID, ka duba su a cikin: Musnadul Imam Ahmad da tsarawar Ahmad Shakir, 1/ 156-157.

26-Ahmad, 4/181, da Dabarani a cikin Alkabir, 2/33/1169, haka nan a cikin addu'a a lamba 1436, da ibnu Hibban, a lamba 2424, 2425 (Mawarid), Alhafiz alhaithamy ya ce a cikin Majma'i Al-Zawa'id, 10/ 178: ((Mazajen Ahmad da daya daga Asanid Al-dabarani amintattu ne)).

Kada Ka nunawa makiyana kare kansu, Ka shiyar dani kofofin alkhairai, Ka saukaka min bin shiriyarka, Ka taimakeni akan wanda ya zalince ni, ya Ubangjina! Ka sanyani mai yawan godiya a gareKa, mai yawan ambato a gareka, mai yawan tsoranKa, mai yawan mika wuya a gareka, mai kankar da kai a gareKa, mai yawan kukan tsoranKa, mai komawa gareKa. Ya Ubangijina Ka karbi tubana, Ka shafe zunubina, Ka amsa addu'ata, Ka tabbatar da hujjata (akan makiyanka), Ka shiryar da zuciyata, Ka dai-daita harshena, Ka fitar da kullin kirjina.” [27]

74 “**Ya Allah** Ubangiji! Mu muna rokonKa daga alkhairin abinda annabinka Muhammad-tsiar da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya rokeka, kuma muna neman tsarinka daga sharrin abinda annabinka Muhammad-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya nemi tsari daga gare shi, kuma Kaine abin neman taimako, isuwa tana gareka, babu wata dabara, babu wani karfi sai ga Allah.” [28]



27-Bukhari a cikin Al'adabul Al'mufrad, a lamba ta: 664, da kuma 665, da Abu Dawud, a lamba ta: 1510, 1511, da Tirmizi a lamba ta: 3551, da ibnu Majah, a lamba ta: 3830, da Ahmad 1/127 a Hakim; kuma Al-zahabi ya inganta shi 1/519, kuma Albany ya inganta shi a cikin Sahihu Abi Dawud, 1/414, hakanan kuma a cikin Sahihul Al-Tirmizi, 3/178.

28- Tirmizi, a lamba ta: 3521, da ibnu Majah, a lamba ta: 3846, da Ma'anarsa, kuma Tirmizi ya ce: ((Wannan Hadisi ne kyakkyawa Garibi)), Albani ya raunana shi, a cikin Dha’ifin Tirmizi, shafi 387.



75 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinka daga sharrin jina, da kuma sharrin ganina da sharrin harshena da sharrin zuciyata, da sharrin maniyyina.”[29]

76 **“Ya Allah,** ina neman tsarinKa daga kuturta mai sanya fararen taba, da hauka da kuturta mai sanya daddatsewar yatsu da kuma munanan cututtuka.”[30]

77 “**Ya Allah** Ubangiji! hakika ni ina neman tsarinKa, daga dabi'u da ayyuka da soye-soyen zuciya ababan ki.”[31]

78 **“Ya Allah Ubangiji! lalle Kai mai yawan afuwa ne, mai yawan karamci, Kana san afuwa Ka yi min afuwa.”**[32]

29- Abu Dawud, a lamba ta: 1551, da Tirmizi, a lamba 3492, haka nan Nasa'i a lamba, 5470, da waninsu, kuma Albany ya inganta shi, a cikin Sahihul, Tirmizi, 3/166, kuma Nasa'i ya inganta shi, 3/1108.

30- Abu Dawud, a lamba ta: 1554, da Nasa'i, a lamba ta: 5493, da Ahmad, 3/192 kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihun Nasa’i 3/1116, da Sahihut Tirmizi 3/184.

31- Tirmizi, a lamba 3591, da ibnu Hibban, a lamba 2422 (Mawarid), da Hakim, 1/532, da Dabarani a cikin Al-kabir, 19/19/36. kuma Albany ya Inganta shi a Sahihut Tirmizi, 3/184.

32- Tirmizi, a lamba ta: 3531, da Nasa’i a cikin Al-kubra, a lamba ta: 7712, kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihut Tirmizi, 3/170.

79 **“Ya Allah** ni ina rokanKa aikata alkhairai, da barin ababan ki, da san miskinai, kuma Ka gafarta min, Ka ji kaina, kuma idan ka yi nufin fitinar wasu mutane, Ka karbi raina ba tare da anfineni ba, kuma ina rokanka, sanka, da san wanda yake sonka, da son aikin da zai kusantar dani zuwa sanKa.” [33]

80 **Ya** Allah ina roƙonKa dukkan alheri, a yanzu haka da anjima, abin da na sani daga gare shi, da abin da ban sani ba, kuma ina neman tsarinKa daga dukkan sharri a yanzu haka da anjima, abin da na sani daga gare shi da abin da ban sani ba*.



33- Ahmad ya fitar da shi da lafazinsa, 5/243 da Tirmizi, a lamba ta: 3235, da makamancinsa, kuma ya ce: na tambayi Muhammad bin Isma'il- yana nufin Bukhari- sai ya ce: (wannan Hadisi ne kyakkyawa Ingantacce)), a karshen Hadisin -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:((hakika ita gaskiya ce, ku karanceta kuma ku koyeta), da Hakim 1/521, kuma Albany ya inganta shi a cikin Sahihut Tirmizi, 3/318.

Ya Allah ina roƙonKa mafi alherin abin da bawanKa kuma AnnabinKa ya roƙeKa, kuma ina neman tsarinKa daga sharrin abin da bawanKa kuma AnnabinKa ya nemi tsarinKa da shi, ya Allah ina roƙonKa aljanna da abin da yake kusantota na magana ko aiki, kuma ina neman tsarinKa daga wuta, da abin da yake kusantota na magana ko aiki, ina rokonKa Ka sanya dukkan hukuncin da Ka hukunta gare ni ya zama alheri.” [34]



34- Ibnu Majah, a lamba ta: 3846, da lafazinsa, da Ahmad, 6/134, lafazin kari na biyu nashi ne, da Hakim kuma ya ingantashi, Al-Zahabi ya wafaka mishi, 1/521, lafazin karin farko nashi ne, kuma Albany ya inganta shi a cikin Sahihul ibnu Majah, 2/327.



81

“Ya Allah Ka kiyayeni da musuluci ina tsaye, Ka kuma kiyayeni da musulunci ina zaune, Ka kiyaye ni da musulinci ina kwance, kada Kasa makiyi ya yi min dariya, ko mai hassada. Ya Allah ni ina rokanka dukkan alherin da taskokinsa yake a hannunKa, ina kuma neman tsarinKa da dukkan sharrin da taskokinsa suke a hannunka.” [35]

82 **Ya (Allah** Ka kaddara mana tsoranka abinda zaka tsare da shi tsakaninmu da tsakanin sabonka, Ka kuma (kaddara mana) daga biyayyarKa abinda zaka isar damu da shi AljannarKa, kuma daga yakini abinda zaka saukaka mana dashi masifun duniya, ya Allah, kuma Ka sanya mu masu jin dadi da jinmu, da ganinmu, da karfinmu matukar Ka rayamu, Ka sanyasu masu wanzuwa a garemu (zuwa mutuwa),

35- Alhakim, 1/525 kuma Zahabi ya inganta shi, Albani kuma ya kyautata shi, a cikina al-jami'i, 2/398, da Silsilatul Ahadis Sahiha, 4/54, a lamba 1540.

Ka sanya ramuwarmu akan wanda ya zalincemu, Ka kuma taimakemu akan wanda ya ki mu, Kada Ka sanya masifarmu a addininmu, Kada ka sanya duniya (ta zama) ita ce mafi girman manifarmu, ko matukar tunaninmu (damuwarmu), kuma Kada Ka dora mana wanda ba zai jikanmu ba.”[36]

83 **“Ya Allah** ina neman tsarinka daga ragwantaka, kuma ina neman tsarinka daga rowa, kuma ina neman tsarinka da amaidani zuwa makaskanciyar rayuwa, ina kuma neman tsarinka daga fitinar duniya da azabar kabari.”[37]



36-Tirmizi a lamba ta: 3502, da Hakim, 1/528 Zahabi ya inganta shi, kuma Albany ya kyautata shi, a cikin Sahihul Tirmizi, 3/ 168, da Sahihul Jami’i, 1/400.
37- Bukhari, a lamba ta: 3822.

84 **“Ya Allah** Ka gafarta min kura-kuraina, da jahilcina, da wuce gona da iri na a cikin lamarina, da abinda kai ne mafi sani dashi fiye dani, ya Allah Ka gafartamin kakacina (sakin bakina) da kokarina (gaskena) da kuskurena, da gangancina, dukkan hakan na gareni.”[38]

85 **“Ya Allah,** na zalunci kaina zaunci mai yawa, kuma babu mai gafarta zunubai sai Kai, ka gafarta mini da gafara daga gareKa, kuma ka yi mini rahama, lallai ne Kai Mai gafara ne, Mai jin ƙai.”[39]



38-Bukhari da Muslim: Bukhari, a lamba ta: 5398, Muslim kuma a lamba ta: 2719.

39- Bukhari da Muslim: Bukhari, a lamba ta: 834, Muslim, a lamba ta: 2705.

86 **“Ya Allah** gareKa na miƙa wuya, kuma da Kai ne na yi imani, gareka ne na dogara, gareKa ne na dawo, saboda Kai ne na yi husuma. Ya Allah lallai ni ina neman tsari da buwayarKa, babu abin bautawa da gaskiya sai Kai (kada) Ka ɓatar da ni, Kai ne Rayayye wanda ba zai mutu ba, aljanu da mutane kuwa zasu mutu.”[40]

87 **“Ya Allah** ina rokonka abubuwan da suke kawo rahamarka, da dalilan gafararka, da aminci daga kowane zunubi, da ganima daga dukkan aiki na kwarai, da nasarar Aljanna, da kubuta daga wuta.”[41]

40-Bukhari da Muslim: Bukhari, a lamba 6398, Muslim kuma a lamba ta: 2719.

41- Alhakim,1/525, ya kuma inganta shi, Zahabi da Baihaki kuma suka yi masa muwafaka a cikin Da’awat, a lamba ta: 206, kuma ka duba Azkar na Nawawi, shafi na 340, hakika Mai tahkikin Abdulkadir Al-Arna'uud ya kyautata shi.

88

“Ya Allah Ka gafartawa muminai (maza) da muminai (mata.”[42]

89 **“Ya Allah** Ka gafarta min zunubina, Ka yalwata mini a gidana, Ka yi mini albarka cikin abinda Ka azurtani.”[43]

90

“(Ya Allah ni ina rokanKa daga falalarKa da jin kanKa domin cewa shi, ba bu mai mallakarsu sai Kai.”[44]



42-Saboda Hadisin Ubadah-Allah Ya yarda da shi-ya ce: Na ji annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: ((Wanda ya nemawa muminai (maza) da muminai (mata) gafara, Allah zai rubuta masa kyakkyawa a dukkanin wani mumini da mumina)). Dabarani a cikin Alkabir, 5/202, a lamba ta: 5092, da 3/334, da kuma lamba ta: 2155, kuma Alhaisami ya kyautata Isnadinsa a cikin Majma'uz Zawa'id, 10/210, kuma Albany ya kyautata shi a cikin Sahihul Jami'i, da lamba ta: 5902, 5/242.

43- Ahmad, a lamba ta: 16599, da lamba 23114, da kum Lamba ta : 23188, da Tirmizi, da lamba ta: 3500, kuma Masu tahakikin Al-musnad suka ce, 27/144, kuma a cikin 38/145: ((kykkyawa ne dan waninsa)).

44-Dabari ya fitar da shi, Haithami ya ce a cikin Majma'i Alzawa'id 10/159: ((Mazajensa Mazajen Sahihu ne, banda Muhammad bin Zayyad shi kuma amintaccе ne)), kuma Albany ya inganta shi a cikin Sahihul Al-jami'i, 1/1278.

91 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinka daga tsufa, da fadowa (daga sama) da rusowar gini, da bakin ciki, da dilmiyewa, da konewa, kuma ina neman tsarinka da Shaidan ya fizgeni lokacin mutuwa, kuma ina neman tsarinka da in mutu ina mai juyawa tafarkinka baya, kuma ina neman tsarinka da in mutu abin sara.”[45]

92 **“Ya Ubangiji ina neman tsarinka daga yinwa, saboda cewa ita tir da abokiyar kwanciya, kuma ina neman tsarinka daga Ha'inci domin cewa shi tir da Abokan sirri.”** [46]

93 **“ Ya Allah** ina neman tsarinka daga gajiyawa da kasala (lalaci) da ragwantaka, da rowa, da tsufa, da rafkana, da talauci da kaskanci, da talauci, kuma ina neman tsarinka daga talauci, da kafirci, da fasikanci, da sabawa gaskiya, da munafinci, da yin aiki da jiyarwa, da riya, kuma ina neman tsarinka daga kurumta, da bebantaka, da hauka, da kuturta mai yanke gaba, da kuturta mai kandarewa, da munanan cututtuka.”[47]



45- Abu Dawud ya fitar da shi da lamba ta: 1552, da kuma Nasa'i, a lamba 5531 da lamba 5532, Albany kuma ya inganta shi a cikin Sahihul Nasa'i, 3/1123, da Sahihu Sunani Abi Dawud 1/425.
46- Abu Dawud ya fitar da shi a lamba1547, da Nasa'i a lamba ta: 5483, kuma Albany ya kyautata shi, a cikin Sahihu Nisa'i, 3/1112.
47- Nasa'i ya fitar da shi, a lamba ta: 5493, da Hakim, 1/530, kuma Albany ya inganta shi, a cikin Sahihul Al-jami'i, 1406, da Irwa'u Al-galil, a lamba ta: 852.



94 **“Ya Allah** ina neman tsarinka daga talauci, da karanci, da kaskanci, ina kuma neman tsarinKa da in zalinta ko azalunce ni.”[48]

95 **“Ya Allah** ina neman tsarinka daga mumunan makwabci a cikin gidan zama, domin makwabcin tafiya (sahara) yana wucewa.”[49]

96 **“(Ya Allah** ni ina neman tsarinka daga zuciyar da bata tsoron Allah da addu'ar da ba'a amsawa, da zuciyar da bata koshi, da ilimin da baya amfanarwa, ina neman tsarinka daga wadannan hudun.”[50]

48-Abu Dawud ya fitar da shi, a lamba 1544, da Nasa'i, a lamba 5475, Albany ya inganta shi a cikin Sahihul Nasa’i, 3/111, da Sahihul Al-jami'i 1/407 kuma Albani ya inganta shi a cikin Mawridul Zam'an, 2/455,
49-Bukhari a cikin Adabul Mufrad, a lamba ta: 117, da Hakim, 1/532, Al-Zahabi ya inganta shi, kuma Nasa’i ya fitar da shi a lamba 5517, albani ya inganta shi a cikin Sahihul Al-jami'i, 1/408, da Sahihul Al-nasa'i 3/118.
50- Tirmizi a lamba, ta: 3482, da Abu Dawud, a lamba 1549, kuma Babban malami Albany ya ingantashi, a cikin Sahihul Al-jami'i, da lamba 1295, da Sahihun Nasa’i, 3/1113.



97 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinka daga mumunan wuni, da mumunan dare, da mumunan lokaci, daga kuma mumunan aboki, da mumunan makwabci a gidan zama.” [51]


98 “**Ya Allah** ina rokanka Aljanna, kuma ina neman tsarinka daga Wuta.”(sau uku) [52]

99 “Ya Allah Ka fahimtar dani addini.” [53]

51-Dabarani ya fitar da shi, kuma Haithami ya ce a cikin Al-zawa'id 10/144: ((Mazajansa Mazajan Bukhari ne)). kuma Albani ya kyautata shi a cikin Sahihul Al-jami'i, 1'411 a lamba ta: 1290.

52- Tirmizi ya fitar da shi a lamba ta: 2572, da Ibnu Majah, a lamba 3340, da Nasa'i a lamba ta: 5536, kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihul Tirmizi, 2/319, da Sahihun Nasa'i, 3/1121, Lafazinsa;((Wanda ya roki Allah aljanna sau uku, Aljanna zata ce: ya Allah Ka shigar dashi Aljanna, wanda ya nemi tsarin wuta sau uku, wuta zata ce: ya Allah Ka tserar da shi daga wuta)).

53- Ruwayar Bukhari da Muslim tana nuni a akan shi a addu'ar Annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ga Ibnu Abbas- Allah ya yarda da su. Bukhari a lamba 143, Muslim kuma a lamba ta: 2477.



100

“Ya Allah ina neman tsarinka da in taraKa da wani alhali ina sani, kuma ina neman gafararka ga abinda ban sani ba.” [54]

101 **“Ya Allah** Ka amfanar dani da abinda Ka sanar dani, Ka kuma sanar dani abinda zai amfanar dani, Ka karamin sani.” [55]

102 **“Ya Allah ina rokanka ilimi mai amfani, da arziki tsarkakke, da aiki abin karba.”** [56]

54-Ahmad ya rawaito shi, 4/403, da ibnu Abi Shaibah, 10/337, da Dabarani a cikin Almu'ujamil Alau'sadh 4/284, kuma Albany ya inganta shi, a cikin Sahihul Altarghib wattarhib.1/19.

55-Tirmizi ya fitar da shi, a lamba ta: 3599, da ibnu Majah, da lamba 259, kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihu Ibnu Majah, 1/47.

56-Ibnu Majah ya fitar da shi, da lanba ta: 925, da Nasa'i a cikin Ayyukan wuni da dare, da lamba102, da Ahmad, 6/294, da 305, kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihu ibnu Majah, 1/152.

103 **“Ya Allah ina rokanka da cewa Kai ne Ubangiji daya tal, abin nufi da bukata, wanda bai haifa ba, ba'a haife shi ba, kuma wani kini bai zamo a gare shi ba, da Ka gafarta mini zunubaina, lalle Kai mai yawan gafara da jin kai ne.”**[57]

104 **“Ya Allah** ina rokanKa lalle cewa godiya ta tabbata a gareKa babu wani abin bautawa da gaskiya sai Kai, {Kai kadai kake, baka da abokin tarayya} {Ya} makagin sammai da kasa, ya ma'abocin girma da karamci, ya rayayye ya tsayayye, ina rokonKa {Aljanna} kuma ina neman tsarimKa daga Wuta.”[58]

105 **“Ya Allah** ina rokanka, saboda ni na shaida cewa kai ne Allah, babu abin bautawa da gaskiya sai kai, kai kadai tal,wanda ake nufa da dukkan bukatu, wanda bai Haifa ba, kuma ba’a haife shi ba, kuma babu wani tamka a gare shi.” [59]



57-Nasa'i ya fitar da shi, da lamba 1300, Lafazin nasa ne, da Nasa’i a cikin Alkubra da lamba 7665, da Abu Dawud, da lamba ta: 985, kuma Albany ya inganta shi, a cikin Sahihut Sunanin Nasa’i , 1/147.

2- Allāhumma inni aʿūdhu bika an ’ushrika bika wa ana aʿlamu wa astaghfiruka lima la aʿlam.

58- Abu Dawud, da lamba 1495, da ibnu Majah, da lamba ta: 3858, da Nasa’i, da lamba 1299, da Tirmizi, da lamba 3544, kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihu Nasa’i, 1/279, kuma a cikin Sahihu Ibnu Majah, 2/329.

59- Abu Dawud, da lamba ta: 985, da Tirmizi, da lamba 3475, da ibnu Majah da lamba, da Ahmad 5/360, kuma Albani ya inganta shi a cikin Sahihu Sunanit Tirmizi, 3/163.

106 **“Ya Ubangijina!** Ka gafarta mini, Ka kuma karbi tubana, lalle Kai Mai yawan karbar tubane Mai yawan gafara.”[60]

107 “Ya Allah da Iliminka na gaibu, da IkonKa a bisa halitta, Ka rayani matukar Ka san rayuwa ce mafi alkhairi a gare ni, Ka karbi raina matukar Ka san mutuwa ce mafi alkhairi a gare ni, ya Allah ni ina rokanka tsronKa a boye da sarari, ina kuma rokanKa kalmar gaskiya a halin yadda da fushi, ina rokanKa tsakaitawa a cikin wadata da talauci, ina kuma rokanKa ni'mar da bata karewa, ina kuma rokanKa sanyin ido da ba ya yankewa, ina rokanKa yarda bayan kaddara, ina rokanKa hutu bayan mutuwa, ina kuma rokanKa dadin duba zuwa fuskarKa, da begen haduwa da Kai, batare da wata cuta mai cutarwa ba, ko fitina mai batarwa ba, Ya Allah Ka kawata mu da adon Imani, kuma Ka sanya mu shiryayyu masu shiryarwa.”[61]



60- Abu Dawud, da lamba ta: 1518, da Tirmizi, da lamba 3434, Lafazin nasa ne, da Nasa'i a cikin Alkubra, da lamba 10292, da ibnu Majah, da lamba 3814, kuma Albani ya inganta shi a ckin Sahihu Ibnu Majah, 2/321, da kuma cikin Sahihut Tirmizi, 3/153.

61- Nasa’i, da lamba 1305, da Ahmad, 4/264, kuma Albani ya inganta shi a cikin Sahihun Nasa’i, 1/280, da 1/281.

108 “Ya Allah Ka azurtani sanKa, da san wanda sansa zai amfanar dani a gurinKa, ya Allah abinda Ka azurtani na abinda nake so, Ka sanya shi karfi a gare ni cikin abinda Ka ke so, ya Allah abinda Ka juyar da shi daga gare ni na abinda nake so, Ka sanya shi dalilin (samun dama) a gare ni cikin abinda Ka ke so.” [62]

109 “Ya Allah Ka tsarkakeni daga zunubai da kurakurai, Ya Allah Ka tsarkakeni daga garesu, kamar yadda ake tsarkake farin tufafi daga datti, ya Allah Ka tsarkakeni da kankara da ruwan sanyi.”[63]

110 “Ya Allah ni ina neman tsarinka daga rowa, da ragwantaka, da mummunar rayuwa, da fitinar kirji (hassada, kulli..) da azabar kabari .” [64]

111 “Ya Allah Ubangijin Jibril, da Mika'il, Ubangijin Israfil, ina neman tsarinka daga zafin wuta, da azabar kabari.”[65]

62-Tirmizi ya fitar da shi, da lamba 3491, kuma ya kyautata shi, Sheikh Abdulkadir Al'arna'ud ya ce: ((shi kamar yadda ya ce ne)), duba Tahkikinsa ga jAMI'UL AL'USUL,4/341.

63- Muslim ne ya fitar da shi, a lamba ta: ta: 476, da Nasa’i, da lamba ta: 400.

64- Nasa’i a lamba 5469, Lafazinsa: (Annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana neman tsari daga abubuwa biyar:

Daga rowa, da ragwantaka, da mummunar rayuwa, da fitinar kirji da azabar kabari)). kuma Abu Dawud ya fitar da shi, da lamba 1539, Arna'uudh ya kyautata shi a Takhrijinsa ga Jami'ul Usul, 4/363.

65- Nasa’i ya fitar da shi, a lamba 1344. da Ahmad 6/61, da Baihaki a cikin Adda'wat, a lamba ta: 109, kuma Albani ya inganta shi a acikin Sahihun Nasa’i 3/1121, da Silsilatul Al-ahadis Assahiha, a lamba ta: 1544.

112 “Ya Allah Ka kimsa mini shiriyata, kuma Ka kare ni daga sharrin kaina.” [66]

113 “Ya Allah ina rokanKa Ilimi mai amfani ina kuma neman tsarinKa daga Ilimin da baya amfanarwa.” [67]

114 Ya Allah Ubangijin sammai {bakwai} Ubangijin ƙasa, kuma Ubangijin Al'arshi mai girma, Ubangijinmu, kuma Ubangijin kowane abu, Mafagin ƙwayar hatsi da kwalfar gurtsu, Wanda Ya saukar da Attaura da Linjila da Alfurƙan,



ina neman tsarinKa daga sharrin dukkan abinda Kake rike da makwankwadarsa, ya Allah Kaine na farko, babu wani abu kafinKa, kuma Kaine na ƙarshe babu wani abu a bayanKa, Kaine zahiri babu wani abu a birbishinKa, Kaine badini babu wani abu koma bayanKa, Ka biyamana bashi kuma Ka wadatamu daga talauci.” [68]

66- Nasa’i ya fitar da shi, Lafazin nasa ne, 5/519 a lamba 3483, Ahmad ya fitar da shi da makamancinsa 33/197, a lamba 19992, da Hakim 1/ 510, shima da makamancinsa, kuma Zahabi ya inganta shi, Masu tahkikin Musanad sun ce dangane da Hadisin Ahmad, 33/197: ((IsnadinSa ingantacce ne a bisa sharadin Bukhari da Muslim)), amma lafazinTirmizi ne , Albani ya raunana shi a cikin Dha'ifut Tirmizi, shafi na 397.

67- Nasa'i ya fitar da shi, a cikin Alkubra, a lamba ta: 3843, kuma Albani ya inganta shi a acikin Sahihu Sunani ibnu Majah, 2/327. Lafazinsa: ((ku roki Allah Ilimi mai amfani, kuma ku nemi tsari daga Ilimin da baya amfanarwa)).

68- Muslim ne ya fitar da shi, a lamba ta: 2713, daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi.

115 “Ya Allah ! Ka hada zukatanmu, Ka gyara tsakaninmu, Ka shiryar da mu tafarkin aminci, Ka tserar da mu daga duffai zuwa ga haske, Ka kuma nisantar damu daga Munana abinda ya bayyana daga garesu da abinda ya buya, Ka yi albarka ga kunnuwanmu da idanuwanmu, da zukatanmu, da matayenmu, da zurriyarmu, Ka karbi tubanmu, lalle Kai Mai yawan karbar tuba ne mai yawan jin kai, Ka sanyamu masu godiya ga ni'imominKa, masu yabonKa akansu, masu karbarsu, Ka kuma cikasu a garemu.” [69]



69-Abu Dawud, da lamba ta: 969, da Hakim, Lafazin nasa ne 1/265, kuma ya ce: ((Ingattacce ne a bisa sharadin Muslim)), Zahabi ya yi masa muwafaka, 1/26, Albani ya inganta shi a cikin Sahihu Adabul Al-Mufrad, da lamba 630.

116 **“Ya Allah !** ina rokanka mafificin roko, da mafificiyar Addu'a, da mafificiyar nasara, da mafificin aiki, da mafificin lada, da mafificiyar rayuwa, da mafificiyar mutuwa, ka kuma tabbatar dani, Ka nauyaya ma'aunaina, Ka tabbatar da Imanina, Ka daukaka darajata, Ka karbi sallata, Ka gafarta kuskurena, kuma ina rokanKa darajoji madaukaka na daga Aljanna, ya Allah ni ina rokanKa mabudan alkhairi da kuma cikarsu, da matattaransu, da farkonsa da sararinsa da boyansa, da darajoji madaukaka na daga Aljanna, Allah Ka amsa, ya Allah ina rokanKa mafificin abinda zan zo da shi da mafi alkhairin abinda zan aikata, da mafi alkhairin abinda ya boyu, da mafi alkhairin abinda ya bayyana, da darajoji madaukaka na daga aljanna, Allah Ka amsa, Ka gyara lamarina, Ka tsarkake zuciyata, Ka katange al'aurata, Ka haskaka zucyata, Ka gafarta min zunubina, ina rokanKa darajoji madaukaka na aljanna, (Ya) Allah Ka amsa, Ya Allah ina rokanKa Ka yi albarka a kaina, da ji na, da ganina, da raina da halitta ta da dabi'una, da iyalaina, da rayuwata, da mutuwata, da aikina, Ka karbi kyawawan ayyukana, kuma ina rokanKa darajoji madaukaka na daga aljanna Allah Ka amsa.” [70]

70-Hakim ne ya fitar da shi, daga Ummu Salamah mar'fu'i, 1/520, Zahabi kuma ya inganta shi, 1/520, da Baihaki a cikin Adda'awat, da lamba 225, da Dabarani a cikin Alkabir, 23/326, a lamba 717.

117 **“Ya Allah** Ka nisantar dani dabi'u ababan ki, da soye-soyen zuciya, da ayyuka, da cututtuka.” [71]

118 **“Ya Allah** Ka wadatar dani da abinda Ka azurtani, Ka yi mini albarka a cikinsa, Ka maye min dukkan abinda ya faku a gare ni da alkhairi.” [72]



119 **“Ya Allah** Ka yi mini hisabi hisabi mai sauki.” [73]

120 **“Ya Allah** Ka taimaka mana a bisa ambatanKa, da godiyarKa, da kyakkyawar bautarKa.” [74]

71-Hakim ne ya fitar da shi, 1/523, kuma ya ce: ((Ingattacce ne a bisa sharadin Muslim)). Zahabi ya yi masa muwafaka, 1/532, kuma Dabarani a cikin Al-mu'ujamul-Alkabir, 19/19 da lamba 36, kuma Albani ya inganta shi a ckin Zilalil Al-jannah da lamba 13.

72- Hakim ne ya fitar da shi, 1/532 ya kuma inganta shi Zahabi, 1/510, daga Ibnu Abbas -Allah ya kara yarda da su - da Baihaki a cikin Al’adab, da lamba 1084, a cikin Adda'wat, 211, Alhafiz Ibnu Hajar ya kyautata shi a cikin Alfutuhat al-rabbaniyya, 4/383.

73-Ahmad ne ya rawaito shi, 6/48, da Hakim, 1/255, kuma ya ce: ((Ingattace ne a bisa sharadin Muslim)), kuma Zahabi ya yi masa muwafaka, 1/55, Nana Aisha-Allah ya kara ya yarda da ita- ta ce: ya yin da ya juyo sai na ce: Ya Manzan Allah menene Hisabi mai sauki? sai ya ce: ((Ya yi duba littafinsa sai ya yafe masa, hakika duk wanda aka tattauna hisabinsa zai halaka, dukkan abinda yake samun mumini Allah Yana kankare masa shi har kayar da ya taka)). Babban malami Albani ya fada akansa, a cikin Mishkatul Al-misbah:(Isnadinsa kyakkyawa ne)).

74-Ahmad ne ya fitar da shi, 2/299, da Hakim, 1/499, kuma ya inganta shi, kuma Zahabi ya yi masa muwakafa, shi lamar yadda suka ce ne, shi a gurin Abi Dawud, da lamba 1524, da Nasa’i a cikin Alkubra, da lamba 9973, kuma Albani ya inganta shi a cikin Sahihul Al-mufrad, da lamba 534.

“Ya Allah ina rokanka Imanin da ba ya juyawa (ridda), da ni'imar da bata karewa, da zama tare da (Manzan Allah) Muhammad-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a cikin madaukakiyar Aljanna ta dawwama.” [75]



75-Ibnu Hibban ne ya fitar da shi (Mawarid) shafi 604, a lamba 2436, daga Ibnu Mas'ud- Allah ya yarda da shi-Maukufi, kuma Ahmad ya ruwaito shi daga wata hanyar daban, 1/386,400, da Nasa’i a cikin Aikin wuni da dare, da lamba 869, kuma Albani ya kyautata shi a cikin Silsilatu al-ahadisu Al-sahiha, a karkashin lamba ta 2301.

122

“Ya Allah Ka kareni sharrin kaina, Ka karfafeni da mafi shiriyar lamarina, Ya Allah Ka gafarta min abinda na boye, da abinda na bayyana, da abinda na yi kuskure, da abinda na yi da gangan, da abinda na sani da abinda ban sani ba.” [76]



123

“Ya Allah ni ina neman tsarinKa daga rinjayar bashi, da rinjayar maƙiyi, da dariyar maƙiya.” [77]

124 “Ya Allah Ka gafarta min, Ka shiryardani, Ka azurtani, Ka bani lafya, ina neman tsarin Allah daga kuncin matsaya ranar Alkiyama.”[78]

76-Nasa’i ne ya fitar da shi a cikin Alkubra, 6/246. da lamba 10830, da Hakim, 1/510, ya kuma inganta shi, kuma Zahabi ya yi masa muwafaka, Ahmad ya fitar da shi, 4/444, Hadisin yana cikin Al-musnad da aka yi tahakikinsa, 33/ 197 da lamba ta: 1992, kuma Hafiz a ckin Al'Isabah ya ce ((Isnadinsa inagattacce ne)) kuma Albani ya inganta shi a cikin Takhrijin Riyadhus Salihin, a ta'alikinsa akan hadisin da lamba ta: 1495.

77-Nasa’i ya fitar da shi, da lamba ta: 5475, da Ahmad, 2/173, kuma Albani ya ingantashi a cikin Sahihun Nasa’i, 3/1113.

78-Nasa’i, da lamba ta 1617, da ibnu Majah, da lamba1356, kuma Albani ya inganta shi a cikin Sahihu Sunanu Nasa’i, 1/356, da kuma Sahihu Ibnu Majah.1/226

125 **“Ya Allah** Ka jiyar dani dadi da jina da ganina, Ka sanyasu masu wanzuwa a gareni, Ka taimakeni akan wanda ya zalunceni, Ka karbarmin fansa daga gare shi.”[79]

126 **“Ya Allah** ina rokanKa tsarkakakkiyar ruywa, da mutuwa madaidaiciya, da makoma (zuwa lahira) ba mai kaskanci ba, ko kunyata ba.”[80]



“Ya Allah ka gafartamin, kajikaina, ka shiryar dani, ka bani lafiya, ka azurtani.” ((... Ka gyarani, Ka daukakani))[81,82] 127

79-Tirmizi ya fitar da shi, da lamba ta: 3681, da Bukhari a cikin Al-adbul Al-mufrad, da Lamba ta 650, da Hakim, 1/523. kuma Zahabi ya ingantashi, kuma Albani ya kyautata shi a cikin Sahihul Tirmizi, 3/188.

80- Hakim ne ya fitar da shi 1/541, da Zawa’idu Musnadul Bazzar 2/442 mai lamba ta: 2177, da Dabarani a Addu’a mai lamba 1435, Haisumi ya ce a Majma’il Zawa’id 10/179: (Isnadin Dabarani mai kyau ne).

81-Muslim, da lamba 2696, da lamba ta: 2697, a cikin wata ruwaya ta muslim: ((lalle wadannan zasu tattarama duniyarka da lahirarka)) a cikin Sunanu ya ce Dawud, da lamba 850: ya ce:

((lokacin da balaraban kauyen ya juya Annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:((Hakika ya cika hannayensa da alkhairi)).

82- ka duba Sunanu Ibnu Majah, da lamba ta: 898. da Sunan Tirmizi, da lamba 284, Ibnu Majah ya inganta shi 1/148. da Sahihut Tirmizi, 1/90.

128 **"Ya Allah** dukkan godiya ta tabbata a gareKa, babu mai damkewa (kuntatawa) ga abinda ka shinfida (yalwata) kuma babu mai shimfidawa ga abinda ka damke (kuntatata), babu mai shiryarwa ga wanda Ka batar babu kuma mai batarwa ga wanda ka shiryar, babu mai bayarwa ga abinda ka hana, babu kuma mai hanawa ga abinda ka bayar, babu mai kusantowa ga abinda ka nisantar, babu kuma mai nisantarwa ga abinda ka kusantar, ya Allah Ka yalwata mana daga albarkatunka, da jin kanka, da falalarka, da arzikinka, ya Allah ina rokanka ni'ima madawwamiya, wacce bata camzawa kuma bata gushewa, ya Allah ina neman tsarinka daga sharrin abinda ka bamu da sharrin abinda ka hanamu, ya Allah ka soyarmana da imani ka kuma kawata shi a zukatanmu, ka sa mana kiyayyar kafirci da fasikanci, da sabo, ka sanyamu da cikin shiryayyu, ya Allah ka karbi ranmu muna muslimai, ka rayamu muna muslimai, ka riskar damu ga salihai ba masu kunyataba ko ababan fitinarwa ba, ya Allah ka tsinewa kafirai wadanda suke karyata manzanninka, suke kuma toshe tafarkinka, ka sanya azabarka a kansu, ya Allah ka tsinewa kafirai wadanda aka bawa littafi, ya Ubangijin gaskiya {Allah ka amsa}."[83]

83-Ahmad da lafazinnsa 3/424, 24/246 da lamba ta: 15492 da abinda ke tsakanin na Hakim, 1/507, 3/23,24. Bukhari ya fitar da shi a cikin Al-adabul al-Mufrad, da lamba 699, kuma Albani ya inganta shi a acikin Takhrij Fiqhus Seerah, shafi na 284, da kuma cikin Sahihul al-adabul al-mufrad na Bukhari, da lamba 538 shafi 259.



129 **“Ya Allah** Ka kara mana kada Ka rage mana, Ka girmamu, Kada Ka wulakantamu, Ka bamu kada Ka hanamu, Ka zabemu kada Ka zaba akanmu, Ka yarda da mu ka sa a yarda da mu.”[84]

130 **“Ya Allah** Ka kyautata halittata, Ka kyautata dabi'una.”[85]

131 **“Ya Allah** Ka tabbatar dani, Ka sanyani shiryayye abin shiryarwa.” [86]

132 **“Ya Allah,** ni ina roƙonKa tabbata a cikin al'amari, da ƙudirin niyya akan shiriya, ina roƙonKa abubuwan da suke wajabta rahamarka, da ayyukan da suke tababtar da gafararKa, ina roƙonKa godewa ni'imarKa, da kyakkyawar ibadarKa,

84-Tirmizi, 5/326, da Hakim, 2/98. kuma ya inganta shi, Shekh Abdulkadr Al-arna'uud a Tahkikinsa na Jami'ul Al-usul, 11/282. da lamba 8847.

85- Ahmad ya fitar dashi 6/68, da 155, da 1/406, da Ibnu Hibbana (2423-Mawarid) da Al-Dayalisi, 374, da Musnadu Abi Ya'ala, da lamba 5075, kuma Albani ya ingantashi a Irwa'ul Ghaleel, 1/115, da lamba 74.

86- Addu'ar Annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ta yi nuni akansa, ka duba: Bukhari, da lamba 6333, haka nan kuma da lambobin 3020, 3936, da waninsu.

kuma ina rokanKa zuciya kubutacciyya, da harshe mai gaskiya, ina roƙonKa daga mafi alkhairin abinda Ka sani, kuma ina neman tsarinKa daga sharrin abinda Ka sani, kuma ina neman gafararKa ga abinda Kake sani, lallai cewa Kaine Masanin abinda ke fake.”[87]

133 **“Ya Allah** ni ina rokanKa (Aljannar) firdausi mafi daukakar Aljanna.”[88]

87-Ahmad, 28/338 da lamba 17114, da 28/356, da lamba, da Tirmizi, da lamba 3407, da Al-Dabarani, a cikin Al-mu'ujam Alkabir da lafazinsa, da lamba 7135, da lamba,7157, da 7175, da lamba7176, da 7177, da 7178, da 7179, da 7180, kuma ibnu Hibban ya fitar da shi, 3/ 215. da lamba 935, da 5/310, da lamba 1975, Al-arna'uud ya kyautata shi a cikin Sahihu Ibnu Hibban 5/312, kuma masu Tahkikiin Al-musnad, sun kyautata shi da hanyoyinsa, 28/338, kuma Albani ya ambace shi a Silsilatul al-ahadisu al-sahiha a cikin mujalladi na bakwai, da lamna ta: 3228. haka nan a cikin Sahihul Mawarid Al-zam'an, da lamba 2416, kuma ya ce: ((ingantacce ne dan waninsa)).

88-An ciro shi ne daga fadar Annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ((...Idan za ku roki Allah, to ku roke shi Alfirdausi, domin ita ce mafi alkhairin aljannah, kuma mafi daukakar Aljannah, samanta Al'arshen Rahman yake kuma daga gareta ne koramun Aljanna suke ketowa)). Bukhari a lamba 2790/ da lamba ta: 7423



134 **“Ya Allah** ka sabunta Imani a zukatanmu**.”** [89]

135 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinKa daga sallar da bata amfanarwa.” [90]

136 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinKa daga mummunan makwabci, daga kuma mata wacce zata sani furfura kafin lokacin furfurar ya yi, ina kuma neman tsarinKa daga Da wanda zai kasance uban gida a gare ni, daga kuma dukiya wacce zata zama azaba a gareni, daga kuma aboki makiri, Idonsa yana kallona (kallon badadi) zuciyarsa kuma tana kiyon (cutar dani), in ya ga kyakkyawa (dana aikata) sai ya binne shi, idan kuma ya ga mummuna (dana aikata) sai ya yada shi)){100}.” [91]

137 **“Ya Allah** kada Ka kunyatar dani ranar Alkiyama.” [92]

89- An ciro shi ne daga Hadisin Abdullahi bn Umar-Allah ya yarda da su-, ya ce: Manzon Allah -tsra da amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce:((Hakika Imani yana tsufa a cikin (zuciyar) dayanku, kamar yadda tufafi yake tsufa, ku roki Allah ya sabunta Imani a zukatanku)), Hakim, 1/4, Zahabi ya yi masa muwafaka kuma ya inganta shi,, Haithami ya ce a cikin Majma'u Al-Zawa’id 1/52: (Dabarani ya ruwaito shi a cikin Alkabir, Isnadinsa kyakkyawa ne)). Albani kuma ya kyautata shi a cikn Silsilatul Al-ahadsil Al-sahiha, 4/113. da lamba ta: 1585.

90-Abu Dawud, da lamba 1549, kuma Albani ya inganta shi a ckin Sunanu Abi Dawud, 1/424.

91- Dabarani a cikin Addu'a, 3/1425, da lamba ta: 1339, Albani ya ce a cikin Silsilatul al-ahadis Al-sahihah, 7/377, da lamba ta: 3137: ((Na ce: wannan Isnadin kyakkyawa ne, mazajensa dukkaninsu daga mazajen Zahabi ne...)).

92- Ahmad a cikin Al-musnad: ((Isnadinsa I ngattacce ne)), kuma Dabarani ya fitar da shi a cikin Al-mu'ujamul Alkabir, 3/20. da lamba ta: 2524, da lafazin ((Ya Allah kada Ka kunyatar dani ranar Alkiyama, kada Ka kunyatar dani ranar debe kauna))

138 **“Ya Allah** ni ina rokanKa lafiya a duniya da lahira.” [93]

139 **“Ya Allah** ni ina neman tsarinka daga Ilimin da ba ya amfanarwa, da aikin da ba'a daga shi, da zuciyar da bata kaskantuwa ga (ambaton Allah) da Addu'ar da ba'a amsawa.” [94]

140 **“Ya Allah** ina neman tsarinKa daga bacin rai ,da bakin ciki, da gajiyawa, da kasala, da rowa da ragwantaka, da rinjayar Mazaje.” [95]



93-ibnu Majah da lamba ta: 3851, kuma Albani ya inganta shi a cikin Sahihu Ibnu Majah, 3/259, haka kuma a cikin Silsilatul Al-ahadisil Al-sahihihah da lamba 1138.

94- Ibnu Hibban ya fitar da shi, da lamba 2440 (mawarid), Albani kuma ya inganta shi a cikin Sahihu mawaridil Al-Zam'an, 2/454, da lamba 2066.

95- Bukhari, a lamba 6363, Anas- Allah ya yarda da shi ya ce: ((Na kasance ina yi wa Manzon Allah-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - hidima duk sa'adda zai sauka, na kasance ina jinsa yana yawaita fadin: ((Ya Allah ina neman tsarinKa...)).



141

“Ya Allah ina neman tsarinka daga azabar wuta, ina kuma neman tsarinKa daga azabar kabari, kuma ina neman tsarinKa daga fitintinu wadanda suka bayyana daga cikinsu da wadanda suka buya, kuma ina neman tsarinKa daga fitinar Jujal.”[96]

142

“Ya Allah ina rokanKa (mutuwar) shahada a tafarkinka.”[97]

96-Muslim, a lamba 2867, a cikinsa: ((ku nemi tsarin Allah daga azabar wuta))... {ku nemi tsarin Allah daga azabar kabari...} zuwa karshensa.
97- Muslim, da lamba ta: 1909, an ciro shi daga fadinsa- tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi: ((wanda ya roki Allah shahada da gaskiya, Allah zai isar da shi matsayin shahidai, koda ko ya mutu akan shinfidarsa)).

143 **“Ya Allah** Ka gafarta min kurakuraina ranar Alkiyama sama da yawan haluttunKa cikin mutane, ya Allah Ka gafarta min zunubina, Ka shigar dani ranar Alkiyama mashiga ta karamci.” (98)

144 **“Ya Allah Ka shiryar dani cikin wadanda ka shiryar, Ka bani lafiya cikin wadanda Ka bawa lafiya, Ka jibinci (lamarina) cikin wadanda Ka jibinta, Ka yi albarka cikin abinda Ka bani, Ka kare ni sharrin abinda Ka kaddara, yadda lamarin yake, wanda Ka so ba ya kaskanta, AlherinKa ya yawaita, Ubangijinmu, kuma girmanka ya daukaka.”** (99)

145 **“Ya Ubangijina!** Ka gafartamin kurakuraina ranar sakamako.” (100)

98- Bukhari da lamba ta: 4323, da Muslim da lamba ta: 2498, an ciro ne daga Addu'ar Annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ga Ubaid Abi Amir, yana daga cikin Addu'arsa-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ga Abi Bardata-Allah ya yarda da su.

99- Ahmad a cikin Al’Musnad, 3/249, da lamba1723, kuma masu Tahkikin Al- musnad suka ce: 3/249 ((Isnadinsa ingattacce ne)). wannan riwayar sakakkace bata da wami dabaibayi da wuturi, kamar yadda ya zo a cikin wata ruwayar daban, a cikin wannan ruwayar, Anas Allah ya yarda da shi ya ce: ((kuma ya kasance yana koya mana wannan addu'ar...)).

100-Muslima, da lamba 214, an ce da annabi-tsira da amincinAllah su tabbata a gare shi- ya Manzan Allah, lalle ibnu Jud'an ya kasance a jahiliyya, yana sada zumunci, yana ciyar da miskianai, shin hakan mai anfani ne ? ya ce: ((Ba zai amfane shi ba, domin shi ba wata rana da ya taba cewa Ubangijina Ka gafarta min kura kuraina ranar sakamako)).



146 **Ina neman gafarar Allah Maigirma wanda babu wani Ubangiji da ya cancanci a bauta masa da gaskiya sai shi, Rayayye tsayayye da kansa, kuma ina tuba a gare shi.”** [101]

147 **“Ya Allah** Ka gafarta min zunubina, Ka tafiyar da fushin zuciyata, Ka tserar dani daga fitunu masu halakarwa.” [102]

148 **“Ya Allah Ka rayani akan sunnar annabinKa-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- Ka karbi raina a kan addininsa, Ka tsareni daga fitintunu masu halakarwa.”** [103]

101-Tirmizi, da lamba ta: 3577, kuma Albani ya inganta shi, a cikin Sahihut Tirmizi, 3/469: ((wanda ya fade shi Allah zai gafarta masa koda a ce ya gudu daga garkon yaki)).

102- An ciro su daga Addu'o'in annabi-tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ga Nana Aisha- Allah ya yarda da ita-: ((Ya Allah Ka gafarta mata zunubinta, Ka tafiyar da fushin zuciyarta, Ka kareta daga fitunu masu halakarwa)) Ibnu Asakir ya fitar dashi da Isnadinsa a cikin (Al'arba'ina fi Manakibi Ummahatil Al- Mu'uminin)), shafi na 85 daga Nana Aisha Allah ya yarda da ita-kuma ya ce: wannan Hadisin kyakkyawa ne daga hadisin Ibnu Al-walid)), a cikin wani bugu kuma na da ban ya ce:((ka tserar dani da shaidan)) maimakon ((daga fitunu masu halakarwa)).

Ka duba Takhrijinsa a gurin Albani acikin al-Dhaa'ifah, da lamba ta: 4207, yana da shahidi daga Ummu Salama- Allah ya yarda da ita- a gurin Ahmad, da lamba ta: 26576, 2/44 da makamancinsa, Lafazinsa: ((Ki ce ya Ubangijin Muhammad wanda yake annabi ka gafarta min zunubina, ka tafiyar da fushin zuciyata, ka tserar dani daga fitunu masu halakarwa, matukar Ka rayamu)).

Kuma Haithami ya kyautata shi a cikin Majma'u Al-zawa'id,10/27, da lamba kuma shi a wurin Dabarani acikin Mu'ujamul Alkabir, 23/338, da lamba 785, ba tare da lafazinsa ba,((mutukar ka rayamu)).

Kuma yana da shahid daga Ummu Hani Allah ya yarda da ita ta ce: ((ya manzan Allah, sanar da ni wata addu'a da zan yi, ya ce: ((Ki ce Allah ka gafartamin zunubina..)). Alkharadhi ya fitar da shi da lamba 52, Masawi'ul Akhlak, da lamba ta: 323.

103-Baihaki ya fitar da shi a cikin AlKubra 5/95 daga addu'ar Ibnu Umar maukufi a gare shi, ibnu Mulakkin a cikin Al-badarul Al-munir, 6/309, ya fada yana mai cirowa daga Dhiya`u. (Isnadusa mai kyau ne)). Ibnu Mas'ud -Allah ya yarda da shi ya ce: ((kada dayanku ya ce: ya Allah ni ina neman tsarinka daga fitna, babu wani face yna kunshe da fitna, domin Allah yana cewa: Kadai dukiyoyinku da yayanku fitina ce {Taghabun:15}. dukkanin wanda zai nemi tsari ya nemi tsarin Allah daga fitunu masu halakarwa)).

Ibnu Jarir, ya fitar da shi a Tafsirnsa, 13/475, da lamba 15912, kuma Ibnu Baddal ya ambace shi a cikin sharhinsa a Sahihul Bukhari, 4/13.

“Ya Allah Ka yi Salati ga Muhammad, da Alayen Muhammad, kamar yadda Ka yi Salati ga Ibrahim, da alayen Ibrahim, Hakika Kai abin godewa ne kuma abin girmamawa ne. Ka yi albarKa ga annabi Muhammad, da alayen Muhammad kamar yadda ka yi albarka a bisa annabi Ibrahim da alayen Ibrahim a cikin talkai (hakika kai abin godewa ne kuma abin girmamawa ne.” [104]

Godiya ta tabbabata ga Allah Ubangijin talikai, kamar yadda yake dacewa da girmansa, da girman milkinsa, Ya Allah Ka yi salati da aminci ga annabinmu Muhammad da Alayensa, da sahabbansa, da mabiyansa da kyautatawa zuwa ranar sakamako.



104- Bukhari da lamba ta: 3370, da abinda ke tsakanin baka biyu na Hadisin Abi huraira-Allah ya yarda da shi [a gurin Muslim 405.

تعرف على الإسلام

بأكثر من 100 لغة

موسوعة القرآن الكريم
QuranEnc.com

ترجمات متقنة لمعاني القرآن الكريم بأكثر من (75) لغة

بيان الإسلام
byenah.com

مواد منتقاة للتعريف بالإسلام وتعليمه بأكثر من (120) لغة

موسوعة الأحاديث النبوية
HadeethEnc.com

ترجمات متقنة للأحاديث النبوية وشروحها بأكثر من (60) لغة

ضيوف الرحمن
hajjumrh.com

مواد منتقاة للحجـــاج والمعتمرين و الزوار بلغات العالم

جامع المحتوى الإسلامي للغات
islamcontent.com

مواد إسلامية متنوعة وشاملة بأكثر من (125) لغة

موسوعات وخدمات إسلامية باللغات
s.islamenc.com

للمزيد من المواقع الإسلامية بلغـــات العـــالم